# Wasikar Wani Matashin Jagora

(Daga littafi mai suna "Gina shuwagabanni: Ginnani daga Ruhu na 4, Malcolm Webber")

Ni jagora ne mai tasowa. Na sani kai gogagen jagora ne. Ina ma Allah matukar godiya da ya hada ni da kai cikin rayuwata. Gakiya ina matukar bukatarka!

Da farko dai, ka koya mani Maganar Allah, idan ka yarda. Gama Gaskiya itace rai. Gaskiya na iya canza tunanina. Ta na iya canza rayuwata. Amma ina so ka koyamini wannan Gaskiyar cikin shafewa tare da sakankancewar Ruhu mai Tsarki, ba cikin kalmomi ba kadai. Ka koyarda ni wannan Gaskiyar tare da sakankancewa kuma da iko.

Amma ina rokon ka, kada ka koyarda ni kawai. Ina bukatar ka raba ruyuwarka da ni. Kada ka koyarda ni zurfin tunani kawai. Ka bude zuciyar ka zuwa gareni. Ka yi mini zancen rayuwarka da Ubangiji, nassarori da ka ci da kuma kasawar ka, inda ka fadi. Ka raba komi tare da ni : bege, abubuwanda suka bashe ka, murnarka, abubuwanda suka bata maka da rai.

Bayan koyaswa, ina ronkon ka ka shigo cikin rayuwata da gaskiya. Ina bukatar in san cewa ina da tamani a idonka, in san cewa gurinka ba kawai ka horasda ni ba ne domin wadansu ayyuka kanan ka turani a yakin cikin sojojinka ba. Ina rokon ka Kada ka yi anfani da ni. Ina bukatar sanin cewa kana kauna ta kuna ka tsaye domi na. Ka nuna mani wannan bada kai naka ta hanyoyi daban daban. A duk lokacinda na yi da kyau ka sanar da ni. A lokacinda na yi kuskure ka dora mani nauyin. Ka kwabe ni a cikin kauna da lafazi mai laushi.

Ka bani nauyin tafiyar da abubuwa, idan ka yarda. Abubuwanda bas u fi karfina ba. Wadansunsu ayyuka ne na yau da kulum domin a karfafa halina na mai hidima. Amma ka bani ayyukanda masu tamani wadanda za su fadada tsinkayena tare da taimaka mini cikin haskaka kira wanda na samu. Ka shiya wadannan abubuwa cikin natsuwa domin su taimaka mini cikin ginuwa tare da karfafa ni a koya, girma da dogara ga Allah domin cin nassara.

A lokacinda ni ke cika ayyukanda ka bani, kada ka barni ni kadai. Ka tsaya a gefe na ka kuma karfafa ni. Kada ka yi haka kai kadai, ama ka gina wadansu huldodi kewaye da ni. Ka karfafa sauran ‘yan uwa maza da mata masu karfi cikin bangaskiya a cikin ekklisiya da su dauke ni tamkar da a garesu a cikin ruhaniya. Ka karfafa su koyon yadda zasu habakarda huldodi da ni yadda haka zai kara ginani. Ta hanyar rayuwarsu zan san ma’anar zama cikaken mai bada gaskiya. Ina son ganin haka. Ba wai zaka koyar da ni haka ba kawai amma zan gan wannan. Ina bukatar ganin haka!

Ina bukatar ganin auraraki masu tsarki, koda yake basu rasa kurakurai. A cikin lokaci kalilan zan yi aure. Ina bukatar sanin abinda haka ke bukata da yadda ake yi. Ka koyarda ni cewa ya wajibta miji ya kaunaci mata tasa kamar yadda Kristi ya kaunaci ekklisyasa. Ta wurin shafewa daga Ruhu mai tsarki na koyarwarka wannan ya taba ni. Wannan ya taba ni kwarai har na yi kwalla a lokacinda na ga haka a cikin Litafi Mai Tsarki. Amma ina bukatar ganin haka a cikin rayuwar yau da kulum. Wajibi ne na ga haka. Ina bukatar ganin jama’a na rayuwa a kewaye da ni.

Ina bukatar wadannan jama’a domin tafiya tare da ni a cikin rayuwa. A lokacinda ni ke koya a cikin rayuwa tare da tafiyantarda ayyuka cikin tukurun aiki, ina bukatar sanin cewa ba ni kadai ba ne, amma ina tare da jama’a a kewaye da ni, wadanda sun nace tare da ni, wadanda ke yaba ni tare karfafa ni da kuma addu’a domina. Ta hanyar rayuwarsu zan san yadda zan yi gwagwarmaya da gwadoji a cikin rayuwa. Na san cewa wajibi ne ni tsaya tsayin daka. Ka rigaya ka koyar da ni haka da kyau. Amma ina

bukatar ganin haka. Ina bukatar kasancewa tare da kai a duk lokacinda ka ke ratsa wahalhalu da mawuyatan lokuta. Zan lura da yadda ka ke jurewa. Zan tuna da wannan. Zan kuwa fahimta da kyau.

Don haka idan ka yarda ka tafi tare da ni. Ka bari in lura da kai a lokacinda ka ke gabatarda wadansu hidimomi na jagora. Ina kaunar koyaswarka, amma ina bukatar ganinka ka aikata abubuwanda ka koyar!

Ta wurin tafiya a tare da yin ayyuka a tare, zan koyi zama jagora. Zan lura da kai a lokutanda ka ke daukar kudurori masu tsauri a cikin mawuyatan lokuta. Zan lura da kai a lokacinda ka ke addu'a domin jama'arda ka ke hidimtawa da kuma lokacinda ka ke kuka dominsu. Zan kasance tare da kai a lokacinda ka ke nuna hakuri zuwa ga sauran jama'a. Zan kasance tare da kai a lokacinda ka ke horasda wadanda su ke cikin kuskure. Ta haka ne zan koyi yadda zan yi wannan ni kaina.

Ka lura da rayuwata. Ka taimake ni sanin gurin Allah domin rayuwata tare da banni ayyuka domin ni gabatar. Ka cigaba da neman zarafi domin sani yin ayyuka. Kada ka bar ni ba aiki, zaune a wofi. Kada ka barni cikin shuru, zaune nesa da kai. Ka kama ni tare da ce mani : « Kai zo yaka da na ! zo ka ga gurin Allah. Dubi abinda Allah ke yi. Ko ka iya kasance da tafiya tare Shi ? Duba ! »Ka tabatarda kiranda Allah ya yi mani. Ka tabatarda cewa Allah nada kyakyawan guri domina. Ka kasance a kulluyaume kusa na kana cewa : "I, zaka iya!". Idan na ce: "A'a b azan iya ba", sai k ace "I, zaka iya". Ka fada mini haka tare da kallubalanta ta. Kanan ka tura ni yin haka tare da wadansu a kewaye da ni.

Idan ka yarda ka hadaa hulda da jama'a, abukan hulda, abukan aiki. Ka sa ni hulda da jama'a wadanda zamu taimakawa juna ta wurin cika zuna watau masu baye baye wadanda ni ba ni da. A wani lokaci ka hada da mutanenda ka san ba zamu shiryu ba, sai mun yi rikici. Zamu fara da rishin jituwa har ma abin ya kaimu ga yin fada. Kanan zan ji damuwa. Zan lura da cewa kana kallo na a lokacin wannan rikici, zan kuwa na bashe ka amma sai in ga ka za gu na ba tare ka bata ranka ba. Za kazo gu na cikin natsuwa da biyaya. Za ka ce da ni : « Kai, Zo! Mu dubi al'amura da kyau. Akwai miyagun abubuwa da dama a cikin rayuwarko ? Wannan mu'amala da hulda sun fitar da su. To, yanzu mu tonasu da kyau. »

A baya, ni kan ji tsoron barin wani ya tana wadannan abubuwa na cikin rayuwata, amma ka gina hulda mai karfi tare da ni. Na sani ka na kauna na da alheri, na sani ka dukufa kuwa domina. Ni kuwa zan bude maka ciziyata cikin hatara. Za ka yi addu'a tare da ni ka kuwa binciki wadansu raununuka na cikin rayuwata. Za mu fuskancesu a tare. A cikin labshin hali, sai ka karfafa ni domin yima wadanda suka yi mini laifi gafara. Za ka jagorance ni domin fitar da dacin zuciya da nukura. Za ka kuwa taimakeni fahimtar wannan rikici da ni a cikin hulda da sauran jama'a, zaka nuna mani ba wannan hulda ba ce ta hadasa rikici a cika amma ta bada dama ga miyagun halayena su bayanarda kansu.

A lokacinda ka ke aiki kan wadannan abubuwa tare da ni, zan fahimci yadda Allah ke aiki a ciki na a lokutan jaki. Ya bari ni shiga wuta. Zan kuwa tuna da koyaswarda ka bani kan wadannan abubuwa tun daga wasikar Bitrus ta farko. A yanzu ina su a cikin rayuwata. Wadansu iyaye zasu kara karfafa wadannan dabi'ar tafiya cikin gaskiya da adalci a cikin rayuwata.

Ta wurin fuskantar dukan wadannan abubuwa tare da mika kai ga Gaskiya da Allah, ta wurin wadannan huldodi masu karfi da karfafawa da sun taimake ni kwaran gaske, tare da dukan mawuyatan kallubalai da tsanani a cikin rayuwa, Allah zai canza ni. Zan fi jin walwala. A haka ne zan ji na fara koyon cikaken ainahin rayuwar Kristanci da jagoranci, ba wai rukuni ba kawai. Ba kuwa « wadansu abubuwa ba kawai » da wani ke dubi da tamani. Ina cikin fahimtar gaskiyar abubuwanda ke wakana tare da ganinsu. Zan ga lalle rayuwata na cikin canzawa. Gaskiyar Maganar Allah na cikin canza ni ta ikon Ruhu a cikin

wani iyali da ke kewaye da ni da kaunarsa, wanda ke ciyarda ni a ruhaniyance wanda kuma ke jin yanada nauyin ginuwata, a duk lokacinda na fuskanci kalubalan rayuwa. Ta haka ne zan san Allah.

Zan ga haka a cikin rayuwarka da cikin rayuwar sauran jama'arda ke kewaye da ni, wadanda su ka nace tare da ni. Zan koyi yin addu'a, saboda zan lura da yadda ka ke addu'a. Zan lura da kai a lokacinda ka ke yabon Allah. Ta hake ne zan fahimci ma'anar « yabon Allah ». Zan gani a cikin maganar Allah wannan wahayi mai kayatarwa wanda ya ke bayanarda cewa an halice ne domin yabon Allah. Zan fahimci wannan. Haka kuwa zan yi domin zaka karfafani cikin yin wannan. Zan san ta yaya zan yi haka, domin na ga yadda kai ka ke yi. Ta wurin yabon Allah, zan dandana ikon Ruhu Mai Tsarki wanda ke kawo canji. Zan kai ga sanin Sa. Zan koyi sadaukar masa da zuciyata, zan kan ga gane Shi; in kuwa gane Shi. Zan san Allah. Zan kuwa sani kyakyawan tunani game da Allah.

Zan fahimci ma'anar samun abokanai saboda zan sami abokanai. Zasu kaunace ni, su kuwa kasance tare da ni koma a lokacinda na yi abinda ba daidai ba. Zaku kasance domina. Zan fara nazari kan koyaswarda ka yi mani, wadda ke cewa Allah ba zai taba yashe ni ba. Zan ga ma'anar abinda ka koyarda ni game da annabi Usaiyah wanda ya rike matarsa cikin gaskiya, ko da shi ke ba ta rike amana ba. Allah kuwa ya ce jama'arsa, « A haka ne na ke tare da ku, ba zan taba yashe ku ba. » Zan tuna a lokacinda ka koyarda ni haka, yadda na zi dadi kwarai, abu mai kayatarwa yana nan tare da ni, har ma na yi kwalla. Amma, a yanzu zan ga haka a cikin hanya mafi karara, mafi kyau, saboda na lura da kai a cikin yin haka. Na fahimci Litafi Mai Tsarki, ama ban san da me wannan ya yi kama ba a cikin rayuwar yau da kulum. Yaya wannan ke wakana ? Ina da tambayoyi da dama. Amma a yanza ka kawo mani amsoshi, ba wai kawai ta wuran koyaswowinka ba, amma har ta wurin rayuwarka. Sabili da ina ganin haka, na kuwa fahimta. A da ina tunanin sanin haka, ta wata hanya daban. Amma a yanzu ne na san wadannan abubuwa cikin hanya mafi kyau. Dukan rayuwata kuwa ta canza.

A cikin dukan lokutan wahala, ba zan kasance ba ni kadai ba, za ka kasance kusa da ni. Na san kiran ka ne kawai zan yi. Idan na kwankwasa a kofarka, zaka bude mani. Ba kuwa kawai idan na zo gun ka ba ; amma kai ma za ka zo gu na za ka kuwa dora mani nauyin dukan abubuwanda na yi. Ko ma na kan so in boye ko kuma in gugu a wani lokaci, ba za ka barni ba. Haka kuwa ba tare da nuna iko ba, amma cikin laushin hali z aka zo gun a. Za ka ce: “Zo, mu dubi wannan matsalar, mu bincike ta a tare. Za ka iya cin nasara. Mu kai kukanmu gun Allah a tare. A duk lokcinda muke fuskantar wahalhalu da tasanani, mu zuba ido ga Allah, tare ganin Hanun Sa cikin rayuwarka. »

Ta wuran lura da kai zan koyi ma'anar aiki da jama'a. Zan koyi yin aika da mutane masu dakin kai. Zan kuma koyi yin aiki da mutane masu tsatsauran hali. Zan koyi ma'anar aure mai tsarki. Saboda za kai ni ganin abubuwanda ke wakana a cikin rayuwar aure. A lokacinda ni ke tunanin na sami matata za ka taimakemu. Zaka saka mu yin hulda da iyalai wadanda ke da karfi, za kuwa su raba rayuwarsu da kokowarsu tare da mu a cikin hanya mai haske.

Zan ga yaudara da kadayin kayan duniya sun bace a cikin rayuwata. Gaskiya zata canza rayuwata. Ikon Ruhu Mai Tsarki zai canza ni. Wannan al'uma mai kauna zata canja ni, a lokacinda mu ke tafiya a tare a wurin koya, wahalhalu da kalubalan rayuwa. Allah zai ginarda cikaken tsarki a cikin rayuwata, zai maida ni mutun kamili – ba wai kawai mutun wanda ya san abubuwa kyawawa ba, mutun wanda zai yi abubwa masu kyau a lokacinda a ke kallon sa ba, amma zan kasance cikaken mutun kamili, saboda ka sifantarda rayuwata. Ba ka tsaya ba kamanai. Ka sa ni koyon abubuwa da suka sa na fitarda abubuwanda ke cikin zuciyata. A lokacinda dukan wadannan abubuwa ke fita daga zuciyata, kana nan kusa da ni domin taimako na fahimtar su a cikin haske Gaskiyar Maganar Allah tare da mika kaina a gare shi, tare saukarda da su ga Ubangiji. Na kuwa karfa alharinsa cikin tawali'u – ba kawai jin

zantutuka game da Alherinsa ba, amma karbar alherinsa. Akwai canji a ciki na, an sami cikaken halin kamilci. Na sani ba a haife ni da rishin aibi, na sani kuwa ina da aibi ba kuwa zan kasance ba da rishin aibi saboda idn na dube ka zan ga akwai kasawa. Na kuwa al'amari na da naka duk daya ne, ba banbanci. Amma na san zan ci nasara saboda na haka a cikin rayuwarka.

Ina son zama kamarka. Cikin lura da kai yadda ka ke neman gurin Allah domin rayuwarka da kuma makomar ekklisiya, cikin dubar ka ka na yin haka, wannan zai taba zuciyata, saboda na ga zuciyarka ta tabu. Zan ga juyayinka, tsinkayenka. Tare da ganin yadda ka ke sadaukarda rayuwarka zan ji karfin sadaukarda tau. Ta dalilin ganin yadda ka ke juyayin batatun rayuk, tare da nuna zuciyar Yesu, zuciyata zata canza.

Zan lura da kai a lokacinda ka kokarin magance muyatatun matsalolin rayuwa da na aiki. Zan ga ba ka damu ba. Ama ka tunkari wadannan wuyatatun matsaloli da karyayar zuciya a cikin zurfin neman fuskar Allah . Zan ga ka na yin haka. Zan mika kai na ga lura da kai. Zan ga yadda ka ke fuskantar wadannan wahalhalu, tare da daukan kuduri da cewa : « Gashi zamu tafi. ». A kalkashin aikin Ruhu Mai Tsarki, zaka kafarda kyakyawan jagoranci. Wannan zai taba ni. Zan tuna da wannan cikin dukan rayuwata. Zan koyi yin haka ni kai na, ba tare da lura ba zan yi koyi haka. Zan sami kaina cikin mawuyacin hali, abin farko da zan yi shi ne neman fuskar Allah – saboda haka kai ma ka yi. Na sha ganin kana yin haka sau da dama. Zan yi haka sau da dama ba tare da na lura ba. Duk yadda a ka yi na san cewa karfin tunaninka da kuma daukan kudura za su batar da launinsu a kan abinda ni ke. Zan ni habakarda wannan karfin tunani. Ba wai kawai domin tunani ba, amma harda aikatawa. Na ga kana yin haka. Na lura da kai a lokuta da dama inda kowa ya tsorata da rishin daukan kuduri. Amma kai ta dauki nauyin yin haka. Ba ka zabi biyar hanya mafi sauki ba. Ka dauki nauyinda ke kanka duk da wahalar yanayi. Zan ga kana yin haka sau da dama. Ba kula cewa ba ta dalilin lura da kai yin haka wannan zai sami nasaba a cikin rayuwata ba. A yanzu zan yi haka, sabili da ta hanyar koyaswarka, ka canza ni. Ta wurin nuna mani hanyar Allah sau da dama, ka canza rayuwata. Ta wurin misalinka da cudanya tare da kai, ka canza ni, ta dalilin tafiya tare da kai a cikin mawuyatan yanayi da kalubalan rayuwata.

Kanan zan ga lalle ka bani zarafi domin hidimtawa wadansu kamar yadda ka yi – inda zan zama masu kamar yadda ka zama a gareni.

Wata rana zan jama'a na jira na domin jagoranci. Zan san cewa Allah ya tayarda ni, ya kuwa shiryas da ni domin jagorantar jama'arsa. Ta wurin rayuwar wadanda ke kewaye da ni, ta wurin kasancewar Sa, ta wurin Maganarsa da abubuwanda na koya a cikin rayuwa ; Allah ya canza ni, ya shiryasda ni tare daa kuwa gina ni. Na san cewa ba zan bata zama da rishin aibi ba, amma dai a yanzu zan iya cikarda nufin Allah a cikin rayuwata. Zan iya jagoranci. Na zama ginane – na ginu da kyau.

**LeaderSource SGA**
513 South Main St.
Suite 2.
Elkhart, IN 46516

Tel: +1 844 532 3371

Email: info@leadersource.org

Website: www.leadersource.org